# Muhalli na 1: Misalin da ke Nuni ga CVE

A wannan sashe, za ku samu wakili - marar yankewa - na samfurin manunan CVE wanda ke nuni zuwa ga shirin CVE na yanzu na Ofishin CT. Manufar waɗannan manunai shi ne su samar da yanayi mai ƙayatarwa yayin tsara shirin. An rarraba manune ta la'akari da matakan sakamakon shirin CVE ko ta la'akari da abin da aka samar ko sakamako, tare da waɗannan sakamakon da aka rarraba ta la'akari da nau'ukan manune. Dole ne kowace manufar shiri ta ƙunshi a ƙalla manunin abin da aka samar guda ɗaya da na sakamako guda ɗaya domin samun damar gano cigaban shiri da nasararsa.

## SAKAMAKO: Zaɓi ga matakan rungumar matasa da al'ummu da ke cikin haɗari

**Manunan Abin da Aka Samar:**

- Adadin mutanen da ke cikin rukunonin al'umma da ke cikin haɗari waɗanda aka kai gare su ta hanyar ayyukan tallafi
- Adadin lokutan da al'umma da jami'an gwamnati ke haɗuwa domin magance matsalolin al'umma/tsaro (da kuma adadin waɗannan abubuwa da suka shafi al'umma)
- Adadi/kiyasin matasa/mata/maza/mahalarta/waɗanda suka samu horaswar XXXX
- Karuwar ƙiyasin mambobi mabambanta;
- Adadin tattaunawar cikin addinai da na tsakanin addinai da aka shirya
- Kiyasin mutanen da da aka ba da rahoton cewa suna haɗa kai da gwamnatoci domin samar da sauyi

Manunan Sakamako:

- Adadin shirye-shiryen cigaba da aka yi nasarar kammalawa tare da taimakon shirin da ya mayar da hankali kan ci gaban al'umma
- Adadin  ayyukan karan kai da ke da manufofi masu alaƙa da CVE a cikin al'ummu, maƙwabta, ko makarantu masu fuskantar haɗari, da sauransu.
- Sauyi ga adadin rukunin al'umma da ke da tunanin cewa matakan lumana na siyasa na wanzuwa ne domin samun 'yanci da cimma muradu
- Adadin matasan da suka kammala halartar horaswa game da shugabanci sannan suka kasance masu halartar tarukan al'umma
- Karuwar sani/ayyukan fararen hula a tsakanin matasa mahalarta
- Raguwar samuwar rikici a cikin al'ummar da abin ya shafa

## SAKAMAKO: An ƙalubalanci ra'ayoyin 'yan ta'adda da masu tsattsauran ra'ayin ta da rikici a faɗin duniya

**Manunan Abin da Aka Samar:**

- Adadi/kiyasin matasa/mata/maza/mahalarta/waɗanda suka samu horaswar XXXX
- Adadin mahalartan kowane taro ko taron ƙara wa juna sani sabanin adanin da ake tsammani
- Adadin shuwagabanni da ake girmamawa waɗanda ke magana a kan batun tsattsauran ra'ayin rikici
- Adadin matasan da aka kai gare su ta hanyar shirye-shiryen ilimi na radiyo/telebijin
- Kason rukunin al'ummar da abin ya shafa da ke da jagora na addini wanda ya kasance VE
- Kason mutanen da ke sauraron shirye-shiryen lumana da sauƙin kai a TV/rediyo ko adadin masu sauraron shirye-shirye da ke nuna sakonni ba na tsattsauran ra'ayi ba a TV/rediyo.

Manunan Sakamako:

- Kason da ke ƙaruwa na al'ummar da ke ƙallon rikici a matsayin hanyar samar da sauyin rayuwa da ba ta dace ba
- Kason da ke ƙaruwa na mutanen da suka ɗauki ra'ayoyin zaman lafiya/guje wa rikici a matsayin abu mai amfani sannan suke yaɗa wannan sako

- Adadin gidan rediyo/jaridu/kafafen sadarwa da ke samar da shirye-shirye da suka shafi CVE
- Ziyarrori/neman ra'ayoyi/rukunonin bincike/da sauransu sun bayyana janyewar goyon baya ga rukunonin VE, da ayyukansu da ra'ayoyinsu
- Adadin nuna zaɓi na ayyukan shiri a kafafen sadarwa (idan akwai)
- Kason da ke ƙaruwa na al'umma da suke da ra'ayin a inganta hanyoyin sadarwa ga matasa domin tattauna batutuwa masu jan hankali

## SAKAMAKO: Karfin CVE na gwamnati da na fararen hula

Manunan Abin da Aka Samar:

- Adadi/ƙiyasin matasa/mata/maza/mahalarta/waɗanda suka samu horaswar XXXX
- Adadin mahalartan kowane taro ko taron ƙara wa juna sani sabanin adanin da ake tsammani
- Adadi/kason jami'an tsaro/jami'an gidan yari da aka ba wa horaswa a fannin koyar da haɗin kai da gyaran hali
- Adadin tallatawa, ayyuka, ko sauran shirye-shirye da suka shafi CSO CVE

Manunan Sakamako:

- Wani adadi na tsofaffin/tubabbun VE da ke samar da shawarwari ga firsinonin da ake ƙoƙarin gyara wa halayya
- Adadin CSO da suka samu ƙaruwar damar biyan bukatu da al'umma ke da su
- Adadin firsinoni da aka samar wa ayyuka, ƙwarwa, horaswa, ilimin boko ko na sana'a da sauransu kafin ko lokacin fito da su daga gidan kaso
- Kason mambobin ma'aikatun gwamnati, na kuɗi, da na fararen hula da suka fara haɗa kai da juna
- Sauyi a kason mutanen da abin ya shafa da ke da ra'ayin cewa a) gwamnati da b) fararen hula suna aiki domin inganta rayuwar al'umma/rukononin da abin ya shafa
- Ziyarta, shiga da shirya tarurrukan ƙara wa juna sani na CVE
- Sanya hannun ƙasashen ƙetare abokan harƙalla a takardun da ke zayyana alfanun CVE

# Cikakken Jerin Sunayen Manunai da Aka ba da Shawarar Amfani da su

## SAKAMAKO: Zaɓi ga matakan rungumar matasa da al'ummu da ke cikin haɗari

| | |
|---|---|
| Mizanin ɓacin rai ko fushi game da a) gwamnati; da b) al'umma baki ɗaya sakamakon wariya ga al'umma marasa rinjaye na rukunin da abin ya shafa. | Kason mutanen da suka ba da rahoton cewa gwamnati a matakin ƙasa na la'akari da ra'ayoyin mazaunanta yayin yanke hukunci game da al'amura |
| Tattaunawa a cikin rukunonin bincike tare da matasa game da yadda su da abokansa ke kashe lokacinsu (misali ina suke zuwa shaƙatawa, me suke aikatawa tare) | Kason mahalarta tattaunawar addinai da suke bayyana cewa suna da ra'ayin sake gudanar da tattaunawa tare da mabiya waɗansu addinai a daban |
| Tunanin cewa a) ƙasar; da b) al'umma baki ɗaya ba su damu da walwalar rukunin mutanen da abin ya shafa ba | Kason mahalarta tattaunawa game da addininsu da suke bayyana cewa suna da ra'ayin sake gudanar da tattaunawa tare da waɗansu mabiya addininsu |
| Adadin shirye-shiryen cigaba da aka yi nasarar kammalawa tare da taimakon shirin da ya mayar da hankali kan ci gaban al'umma | Kason rukunin al'umma da ke da tunanin cewa matakan lumana na siyasa na wanzuwa ne domin samun 'yanci da cimma muradu |
| Adadin  ayyukan karan kai da ke da manufofi masu alaƙa da CVE a cikin al'ummu, maƙwabta, ko makarantu masu fuskantar haɗari, da sauransu. | Kason rukunin da abin ya shafa da ke shafi sama da awanni X wajen aiwatar da ayyukan ci gaba da suka shafi zamantakewa, al'ada, ko wasanni da kuma waɗanda ke nuna sha'awa ga wannan abu (misali, wasanni, ƙungiyoyin matasa, aikin sa-kai; abu mai wahala ne a fahimci wanda ya ɗauki nauyin aikin) |
| Kason 'yan ƙasa da ke yankin da abin ya shafa waɗanda suka gamsu da hanyoyin yanke hukunci (waɗanda ke kebance ta fuskar shekaru da yankin da abin ya shafa) | Kason matasa da ke bayyana cewa shugabannin al'umma na girmama ra'ayoyinsu |
| Kason shugabannin al'umma (gwamnati, shugabannin gargajiya, kasuwanci, farar hula) da suke ba da rahoton gamsuwa da damarmakin da ake samar wa matasa da suka haɗa da ta fuskar wasanni/zamantakewa/al'ada | |

Kason mutanen da ke ba da rahoton aminta da gwamnatin gunduma, gwamnatin yanki, da gwamnatin ƙasa

Karuwar sani/ayyukan fararen hula a tsakanin matasa mahalarta

Adadin matasa da ke ba da rahoton ƙarancin matsaloli da karuwar amincewa da hukumomin gwamnati

Adadin matasa da ke ba da rahoton cewa ƙungiyoyin matasa sun fi tallafa musu da kuma wakiltarsu

Adadin matasa/wasanni/da sauransu, ƙungiyoyin da aka buɗe

Kaso mai sauyawa na al'ummar da ke da ra'ayin cewa jagoranci da ɗorawa bisa hanya sun taka rawa matuƙa wajen taimaka musu game da keɓantattun matsalolin da suka shafe su

Kason 'yan ƙasa da ke da hannu cikin yanke hukunci

Kason 'yan ƙasa da ke nuna cewa matasa/ƙungiyoyin matasa na ba da muhimmin taimako ga al'umma

Kason shugabannin al'umma da ke nuna cewa matasa na da sa hannu yadda ya kamata wurin yanke hukunci a cikin al'umma

Kason al'ummar da suka samu gamsuwa game da ayyuka da kayayyaki (waɗanda ke keɓance ta fuskar shekaru da yankin da abin ya shafa)

Kiyasin mutanen da da aka ba da rahoton cewa suna haɗa kai da gwamnatoci domin samar da sauyi

Kason matasa mahalarta da ke jin cewa za su iya jagorancin sauran matasa

Kason mambobin ma'aikatun gwamnati, na kuɗi, da na fararen hula da suka fara haɗa kai da juna

Kason matasa da ke ba da rahoton gamsuwa da damarmakin da suka shafi wasanni/zamantakewa/al'ada

Kason matasa da ke bayyana samuwar sauye-sauye na cigaba da aka samu a cikin al'ummarsu sakamakon halartarsu cikin ayyukan taimakon jama'a

Adadin matasan da suka kammala halartar horaswa game da shugabanci sannan suka kasance masu halartar tarukan al'umma

Kason matasa da ke ba da rahoton kasantuwar ƙarancin matsaloli da yawaitar gamsuwa da hukumomin gwamnati

Adadin mutanen da ke cikin rukunonin al'umma da ke cikin haɗari waɗanda aka kai gare su ta hanyar ayyukan tallafi

Adadin lokutan da al'umma da jami'an gwamnati ke haɗuwa domin magance matsalolin al'umma/tsaro (da kuma Adadin waɗannan abubuwa da suka shafi al'umma)

Adadi/Kiyasin matasa/mata/maza/mahalarta/waɗanda suka samu horaswar XXXX

Adadin mahalartan kowane taro ko taron ƙara wa juna sani saɓanin adanin da ake tsammani

Adadin 'yan ƙasa da ke halartar tarukan tattaunawa na majalisar gunduma ko makamancin wannan da ke ƙaramin mataki

Adadin tarukan al'umma da aka gudanar domin tattauna al'amuran da suka shafi al'amuran ƙaramar hukuma

Adadin mutane a cikin al'umma da ke samun ayyukan shawarwari da jagoranci

Adadin shirye-shiryen taimakon al'umma da matasa suka aiwatar

Adadin zaurukan tattaunawa da aka samar game da muhimman batututwa

Adadin awannin gudanar da ayyukan taimakon al'umma da matasa suka sadaukar

Adadin shirin taimakon al'umma wanda hukumomi daga ɓangarori biyu suka yi haɗin guiwa wajen aiwatarwa

Adadin tattaunawar cikin addinai da na tsakanin addinai da aka shirya

Adadin shirye-shirye da aka kammala da taimakon al'umma

Adadin faɗakarwa game da bayanan al'umma da aka gudanar

Adadin ziyarori da tattaunawa da al'umma wanda jami'an gunduma da na yanki suka gudanar

Adadin matasa da suka samu horaswa na bunƙasa ƙwarewa

Adadin matasa da aka ba wa horaswa a ɓangaren koyon aiki

Adadin matasa da aka ba wa horaswa a ɓangaren koyon aiki kuma suke aiki, misali, kasuwanci, horaswa a fannin sana'a

Kiyasin mutanen da da aka ba da rahoton cewa suna haɗa kai da gwamnatoci domin samar da sauyi

Kason mutane da ke sa hannu wajen magance matsalolin al'umma

Kason mutanen da abin ya shafa da ke nuna cewa sun halarci tarurruka inda suka samu bayanai sannan za su iya bayyana damuwowinsu da abubuwan da suke so

Kason matasa da ake damawa da su a sha'anin ƙungiyoyin matasa/wasanni/wasan kwaikwayo/da sauransu

Kason matasa da ke jin cewe suna shirye da su fara aiki

Kason matasa da ke gudanar da ayyukan da ba dole ba guda ko sama da haka, irin su wasanni, wasan kwaikwayo, sa-kai

Kason matasan da ke shiga ayyukan gina jama'a

Kason matasa (ta la'akari da rukunin shekaru) da ke cewa suna da damar kaiwa ga (tare da shiga a dama da su a) damarmakin cigaban zamantakewa

## SAKAMAKO: An ƙalubalanci ra'ayoyin 'yan ta'adda da masu tsattsauran ra'ayin ta da rikici a faɗin duniya

- Adadin gidan rediyo/jaridu/kafafen sadarwa da ke samar da shirye-shirye da suka shafi CVE
- Adadin awannin samar da bayanan CVE da watsa su da sake watsa su, wanda XXXX ke gudanarwa
- Adadin nuna zabi na ayyukan shiri a kafafen sadarwa (idan akwai)
- Kason da ke ƙaruwa na al'ummar da ke kallon rikici a matsayin hanyar samar da sauyin rayuwa da ba ta dace ba
- Kason da ke ƙaruwa na mutanen da suka ɗauki daidaitattun aƙidu a matsayin abu mai amfani sannan suke yaɗa wannan saƙo
- Ziyarrori/neman ra'ayoyi/rukunonin bincike/da sauransu sun bayyana janyewar goyon baya ga rukunonin VE, da ayyukansu da ra'ayoyinsu
- Kason da ya ƙaru na mutanen da ke da ra'ayin cewa daidaitattun akidu na da amfani da ma'ana
- Adadin shuwagabanni masu kyan hali daidai gwargwado waɗanda ke shiga al'amarin gudanar da shirye-shirye tare da tura saƙonni yadda ya kamata
- Kason da ya ƙaru na al'umma da suke da ra'ayin a inganta hanyoyin sadarwa ga matasa domin tattauna batutuwa masu jan hankali
- Kason da ya ƙaru na mutanen da ke da ra'ayin cewa daidaitattun akidu na da amfani da ma'ana
- Kason da ya ƙaru na limamai, waɗanda a da aka san da cewa sun riƙe (tsattsauran ra'ayoyin rikici, waɗanda suka fi raja'a kan yaɗa saƙonnin da ba sa alaƙa da rikici sannan na zaman lafiya
- Kason mazauna da ke bayyana saƙonnin masu ƙyawun hali daidai gwargwado a matsayin masu jan hankali
- Kason mazauna da ke da ra'ayin cewa bayanai na ƙara samuwa game da zaman lafiya da salama
- Adadin shuwagabanni da ake girmamawa waɗanda ke magana a kan batun tsattsauran ra'ayin rikici
- Adadi/Kiyasin matasa/mata/maza/mahalarta/waɗanda suka samu horaswar XXXX
- Karuwar kason mambobi mabambanta
- Adadin mahalartan kowane taro ko taron ƙara wa juna sani saɓanin adanin da ake tsammani
- Kason da ya ƙaru na limamen da ke suka samu cikakkiyar horaswa sannan suke da ƙarfin guiwar yaɗa saƙon ƙwaurace wa rikici, daidaitawa, da lumana
- Kason mazauna da ke cewa rikici hanya ce mai kyau ta magance matsaloli
- Raguwar samuwar rikici a cikin al'ummar da abin ya shafa
- Adadin shugabannin al'umma da ake girmamawa da ke jawabi game da hanyoyin magance VE sau uku a wata
- Adadin matasan da aka kai gare su ta hanyar shirye-shiryen ilimi na radiyo/telebijin
- Kason mutanen da ke sauraron shirye-shiryen lumana da saukin kai a rediyo/telebijin ko adadin masu sauraron shirye-shirye da ke nuna saƙonni ba na tsattsauran ra'ayi ba a TV/rediyo.
- Kiyasin rukunin al'ummar da abin ya shafa da ke da jagora na addini wanda ya kasance VE
- Tunanin riƙon amana na shirye-shirye daban-daban

## SAKAMAKO: Karfin CVE na gwamnati da na fararen hula

- Kason rukunin mutanen da abin ya shafa da suke da ra'ayin cewa idan aka aikata laifi, to babban mai laifi da zai fuskanci hukunci iri guda ne da ƙaramin mai laifi (ciki har da wakilan ƙasa)
- Kason mutanen da abin ya shafa da ke da ra'ayin cewa za su iya rubuta ƙorafin 'yancin ɗan'adam ba tare da tsoron mummunan sakamako ba; Kason da ke da ra'ayin cewa za su samu adalci ta hanyar tsarin doka
- Sauyi a Kason mutanen da abin ya shafa da ke da ra'ayin cewa a) gwamnati da b) fararen hula suna aiki domin inganta rayuwar al'umma/rukononin da abin ya shafa
- Kason mutanen da suka ce jami'in ɗan sanda ya ci zarafinsu (da baki ko a aikace) a cikin watanni 12 da suka gabata
- Kason da suka aminta cewa 'yan sanda/ jami'an tsaron gidan yari sukan azabtar/doki/muzgunawa wa firsinoni a-kai-a-kai
- Kason rukunin da abin ya shafa da ke da ra'ayin cewa matakan tsaro na muzguna wa fararen hula (da wuya a yi wannan tambayar a wuraren da ke fuskantar danniya).
- Wani adadi na tsofaffin/tubabbun VE da ke samar da shawarwari ga firsinonin da ake ƙokarin gyara wa halayya
- Adadin shirin taimakon al'umma wanda hukumomi daga bangarori biyu suka yi haɗin guiwa wajen aiwatarwa
- Adadin CSO da suka samu ƙaruwar damar biyan buƙatu da al'umma ke da su
- Adadin firsinoni da aka samar wa ayyuka, ƙwarwa, horaswa, ilimin boko ko na sana'a da sauransu kafin ko lokacin fito da su daga gidan kaso
- Adadi/Kason firsinoni da ke ba da rahoton sauyin halayyar 'yan sanda/matakan tsaron gidan yari ga firsinoni

Adadi/Kason firsinoni da ke ba da rahoton ƙaruwar damarmaki na sadarwa/hulɗayya da iyalai (ziyara, kiran waya, da sauransu)

Adadi/Kason firsinoni da ke ba da rahoton ƙaruwar hulɗayyar taimako a ɓangaren zamantakewa (tare da, misali, masu ilimin tunanin ɗan'adam, ma'aikatan zamantakewa, masu sa-ido, shuwagabannin addinai waɗanda ke bayyana saƙonnin zaman lafiya)

Kason mambobin ma'aikatun gwamnati, na kuɗi, da na fararen hula da suka fara haɗa kai da juna

Adadi/Kason jami'an tsaro/jami'an gidan yari da aka ba wa horaswa a fannin koyar da haɗin kai da gyaran hali

Adadi/Kiyasin matasa/mata/maza/mahalarta/waɗanda suka samu horaswar XXXX

Kasashen abokan hulɗa da aka ziyarta, tarurrukan ƙarawa juna sani na CVE na aka halarta ko aka shirya

Kasashen ƙetare abokan harƙalla sun sanya hannu a takardun da ke zayyana alfanun CVE